



Wannan ita ce Delu.
Tana da ’yan uwa
guda shida.



Iyayenta sun ba ta ƙaramar tukunya. Tana son tukunyar.



Wata rana
’yan’uwanta suka
fasa tukunyar.




Da Delu ta rasa tukunyarta, sai ta fashe da kuka.



Delu ta ruga da gudu. Ta hau kan doguwar bishiya.




Iyayenta suka nemi da ta yi haƙuri. Ta sauko daga kan bishiyar.



ʼYanʼuwanta suka yi mata waƙa. "Yi haƙuri ki sauko ƙasa."



Delu ta mayar da waƙarsu abin dariya.




Sannan, ƙawar Delu ta zo. “Yi haƙuri ki sauko ƙasa.” Ta rera waƙa.



Kawar Delu ta ci gaba da waƙa, har sai da ta sauko daga kan bishiya.



Suka tafi gida tare da ƙawayenta.



Kowa yana farin cikin dawowar Delu gida. Delu ta samu sabuwar tukunya.